Ya zowa Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- wani dan leken Asiri daga cikin Mushirikai, kuma yana cikin tafiya

An rawaito daga Salamah Bn Al-akwa’a –Allah ya yarda da shi- “wani dan leken Asiri daga cikin Mushirikai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, kuma yana cikin tafiya, sai ya zauna a wajan Sahabbansa ina zantawa das u, sannan sai ya bace, sai Annabi SAW y ace ku nemo shi ku kasha shi, sai na kasha shi, sai ya bani ganimar Kayansa” a cikin wata riwayar kuma sai y ace: waye ya kasha Mutumin ? sai suka ce: Ibn Al-akwa’a, sai y ace: yana ganimar kayansa baki daya”

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi - Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Wannan Hadisin ya na cikin bayani ne kan hukuncin Musulunci ga wanda yake liken Asiri cikin Musulmai daga cikin Kafirai; saboda Salama Bn Al-akwa’a ya bada labarin cewa: “Wani Dan liken Asiri ya zo wa Manzon Allah SAW daga cikin Mushirikai” ankirawo shi da idon Masu liken Asiri; saboda aikinsa da ido yake yi, kuma shi shi halin Manzon Allah SAW a cikin tafiyarsa sai Dan liken Asiri ya zauna a wajen Sahabbansa yana Magana, sai ya bace sai Manzon Allah y ace ku kasha shi sai aka kasha shi, sai na kasha shi, sai ya bani rabon ganimar da ake bayarwa rabon ganima, kuma a kara Masa akan rabonsa, “Ganimarsa” ai abunda ya kasance akansa na lada da kuma Takobi da aka ambace shi das hi, saboda zai rabashi das hi, kuma zai shiga cikin Ganima: dukkan abunda yake kai na Sirdi da kuma kaya, kuma da abunda yake tare da shi na Dabba da kuma Dukiya, kuma da abun yake daure das hi na Zinare da Azurfa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/2939